# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsa kanin al’umma a Afirka
## Kashi na biyar: Wa zan yarda da shi?


Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu

Wanda ya fassara: Yusuf Idris

Wadda ta tace: Halima C. Schmaling


**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Julie: | ’yar shekara 40 |
| Taron mutane | |
| Mrs. Audu: | ’yar shekara 45 |
| Adams: | ɗan shekara 10 |
| Sherifat: | ’yar shekara 40 |
| Fati: | ’yar shekara 16 |
| Hadiza: | ’yar shekara 30 |
| Ɗan sanda: | ɗan shekara 45 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin wani shiri na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan cin zarafi a nahiyarmu ta Afirka. A shirin da ya gabata, kun ji yadda matar nan, wato Precious, take ta yaba wa sabon saurayinta Kawu Jammo, wai saboda yana kulawa da ɗanta Adams yadda ya kamata. Ashe ba ta san cewa yana ta cin zarafin ɗanta ba ne. A halin da ake ciki kuma Hadiza da ke asibiti ta fara samun sauƙi bayan cin zarafin da 'yan ta'adda suka yi mata ta hanyar fyaɗe, har ya kai ta ga ɓarin cikin da take ɗauke da shi. Ita kuma Fati, ta bai wa mahaifiyarta mamaki bayan ta koma gida hutun ƙarshen mako saboda ta buƙaci cewa tana so ta kasance ita ɗaya. Ita ma dai Fati tana cikin wani hali ne saboda cin zarafinta da malaminta, Malam Tanko, ya yi.

Yanzu me zai biyo baya? Nan ba da jimawa ba za mu ji a cikin shirin na yau wanda shi ne na biyar mai taken "Wa zan yarda da shi?". Za mu faro ne daga babban titin garin inda Julie mai ƙungiyar nan da ke yaƙi da cin zarafin mata ta shirya wata zanga-zangar lumana.

**Fitowa ta 1: Zanga-zangar lumana**

**Julie:** Ba za mu yarda da cin zarafin mata ba!

**Taron mutane:** Ba za mu yarda da cin zarafin mata ba!

**Julie:** Muna son mu ƙwato hakkin mu!

**Taron mutane:** Muna son mu ƙwato hakkinmu!

**Julie:** Muna son mu ƙwato hakkin mu! Jama'a 'yan'uwana, lokaci ya yi da za mu miƙe! Ba zai yiwu a ce a ci gaba da jira ba ko da kuwa na minti ɗaya ne. Dole ne mu kawo ƙarshen cin zarafin da ake yi mana. Saboda waɗanda suka shiga hali na cin zarafi da fyaɗe na kokawa ne a ƙwato musu

hakkinsu, suna ta kasancewa cikin ƙunci a kan abin da ya faru da su. Kullum suna kasancewa cikin kunya bayan laifi na kan wasu ne da suka aikata musu wannan mummunan aiki. Dole ne mu goya musu baya don samu musu ci-gaba da gudanar da rayuwarsu kamar yadda suka saba. … Mu yi yaƙi da cin zarafin mata!

**Taron mutane:** Mu yi yaƙi da cin zarafin mata!

**Mai ba da labari:**

A lokacin da Julie take gudanar da zanga-zangar lumana a cikin birni, shi kuma Adams yana tsaye a ofishin malamarshi, wato Mrs. Audu. A 'yan kwanakin nan dai Adams ya daina shiga cikin yara 'yan'uwanshi. Da wuya ya yi magana da wani, ba ya bin irin koyarwar da ake yi musu a aji, sannan sai ya yi ƙoƙarin gaske yake taɓuka wani abu ƙwarai a ajin. Mrs. Audu ta san Adams tun yana ɗan shekaru bakwai. Ta san cewa ba haka yake ba, amma kuma tana da ilimin gane cewa mutum yana da wata matsala. Saboda haka bayan ta ga irin canje-canjen da ta gani a halayyar Adams, sai ta yanke shawarar yin ƙoƙarin gano abin da ke damunshi.

**Fitowa ta 2: A makarantar su Adams**

**Mrs. Audu:** Adams, ina so ka amsa min waɗannan 'yan tambayoyi, saboda yau ma ba ka gama homework ɗin naka ba.

**Adams:** Amma Malama, ki yi haƙuri.

**Mrs. Audu:** Adams, da ba haka kake ba. Amma kar ka damu. To ka yi wannan ɗan kaɗan ɗin kawai, ba komai. Na rubuta tambayoyi uku a kan wannan 'yar takardar. Ina so ka rubuta sunanka a saman takardar. Sannan kuma tambaya

ta farko da nake so ka amsa ne ita ce: Me ka fi son yi a lokacin da ba ka komai? Ka gane? Shin buga ƙwallon ƙafa ka fi so? Ko zane? Ko kuma me? Ka yi tunani sannan ka rubuta amsar. Tambaya ta gaba ita ce: Wane ne babban abokinka? Sannan tambaya ta ƙarshe ita ce: Wane ne ba ka so? Shi ke nan. Zan ba ka ɗan lokaci da za ka amsa, zan dawo nan da 'yan mintuna kaɗan.

**Adams:** A'a! Me na fi son yi a lokacin da ba na komai? Hmm… Na fi son sauraron… a'a! Na bar jin waƙa yanzu, tun… Wane ne babban abokina? Babban abokina shi ne… Wane ne ba na so? Kawu … A'a! Bai kamata in faɗa ba. Idan ba haka ba, ya ce zai yanke min harshena da kunnuwana. Bai kamata in faɗa ba. Bari in goge wannan amsar… Yauwa, haka ma ya fi.

**Mrs. Audu:** To, Adams, ka gama ne?

**Adams:** Na gama, Malama.

**Mrs. Audu:** Yauwa, ai kuwa ka yi saurin gamawa! To shi ke nan. Ba ni takardar.

**Adams:** Ina iya wucewa gida, Malama?

**Mrs. Audu:** Tukuna dai, Adams. Ka tabbata ka gama? Kana iya ƙara lokaci idan kana so.

**Adams:** A'a, na gama. Ina iya wucewa?

**Mrs. Audu:** E, Adams, kana iya tafiya gida. Ka gaishe min da mamanka. Yauwa, kuma ka ce mata ina son ganinta gobe.

**Mai ba da labari:**

Mrs. Audu ta tsaya na ɗan lokaci tana riƙe da takardar Adams da ya amsa tambayoyin nan uku. Daga abin da Adams ya rubuta, ta san cewa akwai wata babbar matsala. A wani wurin kuma, Fati ta koma makaranta kuma kamar yadda ya yi alƙawari Malam Tanko ya sa ta zama na ɗaya a darasin halittar ɗan Adam. Mahaifiyarta da ta kawo mata ziyara ta yi matuƙar farin ciki da irin sakamakon da Fati ta samu.

**Fitowa ta 3: A makarantar su Fati**

| | |
|---|---|
| **Sherifat:** | Fati, ina matuƙar fari nciki da alfahari da ke bisa irin ƙoƙarin da kike yi a makarantar nan. Kin ga yadda kika samu sakamako mai kyau kuwa, musamman ma a *biology*. Da ba kya ƙoƙari a kanshi sosai. Ina ganin ya kamata ki fara tunanin zama likita. |
| **Fati:** | Mama, don Allah ya isa! Ki ƙyale ni da wannan maganar! Tun da kika zo maganar da kike yi ke nan. |
| **Sherifat:** | Lalle Malam Tanko, mai kula da ɗakunan kwananku, ya iya koyar da wannan darasin. |
| **Fati:** | Don Allah ya isa haka nan! Kina ji? Maganar ta ishe ni haka. |
| **Sherifat:** | Haba 'yata, haba Fati! Wai me yake damunki ne? Daga ina faɗan yadda nake alfahari da ke, wannan sakamakon ai abin da za a yi farin ciki da shi ne. Amma kuma na lura da ke, ba kya jin daɗi ko kaɗan. Faɗa min mana 'yata, me yake damunki? Akwai wani yaron da yake damunki a makarantar nan ne? Ni mahaifiyarki ce, ki faɗa min ko ma |

mene ne.

**Fati:** Mama, ina ganin ya kamata ki wuce yanzu. Na kusa tafiya wurin cin abincin dare.

**Sherifat:** Kafin in zo in gan ki na ɗan tattauna da Malam Tanko.

**Fati:** Kun tattauna? A kan me?

**Sherifat:** A kanki mana! Ya ce duk cikin ɗaliban da yake koyarwa ya fi alfahari da ke. Kuma ya ce yana nan yana jiran ya ga kin shiga cikin ƙungiyar wasan motsa jiki ta makarantar.

**Fati:** Ba ni da sha'awar haka.

**Sherifat:** Mene?! Fati, wannan wata dama ce fa da za ki nuna cewa kin iya gudu sosai! Wata dama ce da za ta iya fitowa da ke sosai a wannan harkar.

**Fati:** Na ce ba na sha'awa! Faƙat!

**Sherifat:** Fati, da gaske? Wai me yake shiga cikin kan nan naki ne?

**Fati:** Ba ki gane ba. Ba za ki gane ba.

**Sherifat:** In gane me? Haba Fati! Duk malamanki suna alfahari da ke, kina ƙoƙari sosai a karatunki, me kuma kike so? Faɗa min 'yata.

**Fati:** Mama, ki gai da gida. Sai na zo hutu. Yanzu kam zan je in abinci.

**Mai ba da labari:**

Sherifat ba ta gane wa 'yarta ba. Tana ganin cewa ya kamata a ce Fati ta fi kowa farin ciki a makarantar. Me yake faruwa ne haka? Shin Sherifat za ta gane gaskiyar abin da ke faruwa kuwa? Ita kuma Fati, wa za ta yarda da shi har ta faɗa mai abin da ya faru? Yana da muhimmancin gaske ga waɗanda ake cin zarafinsu ko kuma yin musu fyaɗe, su fahimci cewa ba su kaɗai ba ne. Hadiza na ƙoƙarin shawo kan halin da ta samu kanta a ciki. Likitanta ya ba ta ƙwarin gwiwar cewa ta kai rahoton abin da ya same ta ga jami'an 'yan sanda, kuma ta nemi a ƙwato mata hakkinta. Amma a yayin da ta kai caji ofis ɗin sai ta gane cewa faɗin abin da ya kawo ta nan ba wani ƙaramin aiki ba ne.

**Fitowa ta 4: A caji ofis**

| | |
|---|---|
| **Hadiza:** | Yallaɓai, sannu da aiki! Sunana Hadiza. |
| **Ɗan sanda:** | To sannu Hadiza. Me ke tafe da ke? |
| **Hadiza:** | Na zo ne in yi rahoton wani abu da ya faru ne. |
| **Ɗan sanda:** | To yi sauri ki faɗi. Muna da aiki da yawa a gabanmu. |
| **Hadiza:** | Ɗan sanda, wannan abu mai wahala ne a gare ni. Kuma ni ya shafa. |
| **Ɗan sanda:** | Malama, za ki faɗa min abin da ya kawo ki ko ba za ki faɗa ba? Na riga na faɗa miki cewa muna da aiki da yawa a gabanmu. |
| **Hadiza:** | Yallaɓai, ba ka san irin halin da na shiga ba ne. |
| **Ɗan sanda:** | Ayya, ki yi haƙuri Malama, nan ba zaman makoki ake yi ba. Idan kuka za ki yi sai ki koma waje ki yi. In kin gama kukan |

kuma kin shirya ba da rahoton kya dawo.

**Hadiza:** Ka yi haƙuri, zan daina kukan. To, ni dai yanzu haka daga asibiti nake. Ina… a bakin ruwa ya faru. Ni da ƙawata Jummai mun je ɗiban ruwa, sai ta baro ni a can kafin… kuma da na rage ni kaɗai, sai 'yan ta'adda suka zo kuma… kuma…

**Ɗan sanda:** Sai kuma me ya faru? Ci gaba! A'a! Ɗan dakata, bari in kira ogana. Ya kamata shi ma ya ji labarin nan.

**Hadiza:** A'a, a'a, don Allah kar ka kira shi! Ba ƙaramin ƙoƙari na yi na faɗa maka labarin ba. Ba zan iya faɗa ma kowa da kowa labarin abin da ya same ni ba. Abin yana da ciwo sosai. Zana da ciwo kuma dakunyatarwa.

**Ɗan sanda:** Kin ce sunanki Hadiza ne ko? To saurara ki ji Hadiza, kin zo ne don mu taimake ki. To idan kuwa kina so mu taimake ki, dole ne ki faɗa mana abin da ya faru da ke. Idan har ta kai ga sai mun je kotu. To dole ne fa ki yi ta maimata abin da ya faru. Saboda haka ya kamata ki saba da hakan.

**Mai gabatarwa:**

Da haka kuma muka kammala wannan shiri na yau. Sai dai maimakon jami'in ɗan sandan nan ya tausaya wa Hadiza bisa halin da ta samu kanta a ciki kuma ya keɓe ta gefe ɗaya ta ba shi labarin, sai ya nuna shi labarinta kawai yake jin daɗin ji. Duk waɗanda suka shiga wannan hali na fyaɗe ko cin zarafi sukan sha matuƙar wahala wajen fafutukarsu na neman ƙwato musu hakkinsu. To yanzu me zai faru da Hadiza? Sai ku kasance da mu a shirinmu na gaba. Kuna iya lalubarmu ta adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Ko kuma ku haɗe dam u a mahawarmu ta Facebook.